# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Aljannar Kare – Haɗarin Afkawa Cikin Bashi
## Kashi na shida: Haɗarin dake tattare da kaddarorin jingina

Wanda ya rubuta: James Muhando
Wanda ya fassara: Danlami Bala Gwammaja
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Mai ba da labari: | ɗan shekara 30 |
| Kawu Natanko: | ɗan shekara 45 |
| Zaliha: | 'yar shekara 35 |
| Binta: | 'yar shekara 11 |
| Nana: | 'yar shekara 35 |
| Ali: | ɗan shekara 15 |
| Ɗan daba na 1: | ɗan shekara 45 |
| Ɗan daba na 2: | ɗan shekara 45 |
| Maman Jamila: | 'yar shekara 35 |
| Yallaɓai: | ɗan shekara 50 |
| Jamila: | 'yar shekara 15 |
| Sakatariya: | 'yar shekara 25 |
| Bash: | ɗan shekara 15 |

**Mai ba da labari:**

Masu sauraro, barkanmu da sake saduwa a cikin ofishina. Kuma barka da sake saduwa a cikin kashi na shida na shirinmu na "Ji Ka Karu" mai suna "Aljannar Kare – Haɗarin Afkawa Cikin Bashi" wanda wasa ne a kan matsalolin da ke tattare da cin bashi. Kar dai ku manta sunana Aliyu Bello, kuma ni ne jagoran wannan shiri.

A cikin kashin da ya gabata kun ji yadda baban abokina ya kai shi caji'ofis bayan da ya samu labarin cewa ɗansa ya kwaikwayi sa-hannunsa don ya karɓi bashi. Ita kuma Jamila karyewa ta yi a hannu a lokacin da muke ƙoƙarin tsere wa mai bayar da bashin nan, wato Malam Ado, wanda yake neman sai an biya shi kuɗin da muka ranta. Ni kuma a lokacin na kasa zuwa gida saboda na ga waɗansu mutane da ban yarda da su ba a ƙofar gidanmu. Don haka sai na kwana a cikin garken shanu. To abin da ya biyo baya dai da safe bayan na isa gida ba na wasa ba ne.

**Fitowa ta 1: A gidan su Ali**

**Kawu Natanko:** Yauwa Ali! Gara da na gan ka kuwa. Don kuwa mun daɗe ba mu haɗu ba! Zo ku gaisa da kawun naka Natanko mana! … Ke Zaliha! Ga wannan yaron ya zo!

**Zaliha:** Allah na gode maka. Ali, lafiya kuwa? Kusan shiɗewa na yi saboda damuwa! A'a, warin me nake ji haka? Ke Binta yaya kika tsaya kina kallo? Je ki, ki samo wa ɗan'uwanki ruwan shayi ya sha. Ba kya ganin rawan sanyi yake yi?

**Binta:** Allah Sarki, ɗan yaro! Mama kin san kuwa Ali da abokansa sun sace rediyon Kawu Natanko!

**Zaliha:** Me kike cewa?

**Mai ba da labari:**

Kun ji shaƙiyyiya ko? To, ta tona mana asiri a gaban kawuna, wanda shi ne ke da rediyon da na kai wa Malam Ado a matsayin kadara don karɓar wa Bash rancen kuɗi. Ni ban taɓa tsammanin zan sake ganinsa ba ma saboda tsawon shekarun da muka ɗauka ba mu gan shi ba. Babu wani abin yi illa na ba su labarin ainihin abin da ya faru, tun daga farko har ƙarshe. Kuma sai da na haɗa musu da labarin 'yan dabar nan da suka zo suke jira a ƙofar gidanmu. Ni dai ban sani ba ko kawu Natanko ya gan su lokacin da ya zo. Ashe shi ma bai gan su ba. Na tsaya ina tunanin ko su wane ne, sai kawai na ji babata ta kama kunnena ta nufi gidan su Bash da ni.

**Fitowa ta 2: A gidan su Bash**

**Zaliha:** Ke Nana!

**Nana:** Zaliha, ke ce? Da sassafe haka. Au ashe ma har da Ali. Ni na ɗauka yau Asabar.

**Zaliha:** Kin san kuwa cewa ɗanki yanzu shi ne shugaban 'yan daban garin nan?

**Nana:** Ɗana kuma? Ban gane shi ne shugaban 'yan dabar garin nan ba? Mene ne ya faru?

**Zaliha:** To dai Nana, ki sani cewa ɗanki shi ne ya shirya abubuwan mamakin da suka dinga faruwa a garin nan!

**Nana:** Ni wallahi na kasa fahimtar inda kika sa gaba?

**Zaliha:** Magana fa nake miki a kan Bash! Wai ashe shi ne ya ja wannan shashasha ɗan nawa, suka fara sace-sace a gidajen mutane!

**Ali:** Ni fa Mama ba haka na faɗa ba.

**Zaliha:** Rufe min baki! Faɗa mata duk abin da ka faɗa min. Faɗa mata yanzu-yanzun nan, mara kunya!

**Mai ba da labari:**
Shi ke nan, sai na ba wa Maman Bash labarin yadda abin ya faru tun daga farko. Ni ina ganin babata ta fusata, ashe babar Bash ma ta fi ta fusata. Ba ta yi wata-wata ba sai ta nufi ɗakinsa. Shi kuma Bash da ya ji hayaniyar da ake yi, sai ya ɓace kafin ma ta kai ga ɗakin nasa.
Can kuma da daddare, sai ga Kawu Natanko ya shigo gida da fasasshen hanci. A cewarsa, wai faɗawa rami ya yi. Ni dai kam ban gamsu ba. Washegari sai aka neme shi aka rasa. Daga baya sai muka fahimci cewa akwai wani abu ma da ba a gani ba.

**Fitowa ta 3: A wajen cin abincin dare**

**Binta:** Don Allah, Ali ka yi haƙuri!

**Ali:** Ke, kar ki dame ni!

**Binta:** To ai na ba ka haƙuri!

**Ali:** Na ce kar ki dame ni ko!

**Zaliha:** Kai, ku ci abinci mana! … Ke Binta kin tabbata kin ga kawunku ya fice da jakarsa?

**Binta:** E, amma shi bai gan ni ba. Leƙawa na yi ta wundo na gan shi.

**Ali:** Ai fa sai dai leƙen! Ba ki iya komai ba sai leƙen mutane!

**Zaliha:** Kai Ali, ya isa haka. … Na yi mamakin yadda kawunku zai tafi bai yi sallama da kowa ba, wallahi! … Natanko ne?

**Ɗan daba na 1:** E, ni ne.

**Zaliha:** Kai Aliyu, buɗe wa kawunka ƙofa.

**Ali:** To Mama. … Wayyo Allah!

**’Yan daba:** Kai maza-maza ku koma ciki. Kowa ya koma ya zauna!

**Zaliha/Ali/Binta:** Wayyo Allah! Kai, mun shiga uku!

**Ɗan daba na 2:** Kowa ya yi shiru, kuma kada wanda ya motsa, babu abin da zai same ku! Ina yake?

**Zaliha:** Wane ne?

**Ɗan daba na 1:** Kin san wanda muke nufi. Ki gaya mana ina Jibrin Haruna ya shiga? Kar ki kuskura ki yi mana ƙarya saboda mun gan shi jiya da daddare! Ina yake?

**Zaliha:** Mu ba mu san wani mai suna Jibrin Haruna a nan gidan ba!

**Ɗan daba na 2:** Ke! Kin ga Malama, ki tsaya ki yi tunani kafin ki ba mu amsa. Kina nufin ba ki san mutumin da ke cikin wannan hoton ba?

**Binta:** To ai wannan ba Jibrin Haruna ba ne. Wannan Kawu Natanko ne!

**Ɗan daba na 2:** To yanzu ina yake?

**Binta:** Ya tafi yau da safen nan. Ya koma cikin gari.

**Ɗan daba na 2:** Ke yarinya, ƙarya za ki yi min ko? … Soja!

**Ɗan daba na 1:** Na'am Oga!

**Ɗan daba na 2:** Bincike đakunan nan!

**Ɗan daba na 1:** To Oga! … Ai ba ya ciki, ba ya nan!

**Ɗan daba na 2:** To, ka ga abin?

**Ɗan daba na 1:** Shi ma ban gan shi ba!

**Ɗan daba na 2:** Ke ina abin yake?

**Zaliha:** Wane abu?

**Ɗan daba na 1:** Ina takardar fulotin da Jibrin… Kawu Natanko ya yi alƙawarin zai bayar a matsayin kadarar biyan bashin da ya karɓa daga maigidanmu?

**Mai ba da labari:**
Daga nan dai sai 'yan dabar nan suka yi kaca-kaca da gidanmu, amma kuma ba su samu abin da suke nema ba. Daga baya Binta ta ce, ta ga Kawu Natanko ya đauki wani shuđin ambulan daga wannan durowa. Sun fice dai cikin fushi. To yanzu dai Mama ta rasa takardar mallakar fuloti, wanda daidai yake da ta rasa fulotin nata wanda a kansa rayuwarta ta dogara! Da safe sai ta tafi caji ofis. Ashe dai ba ita kađai ta tafi ba.

**Fitowa ta 4: A caji ofis**

**Yallaɓai:** Maman Jamila, na gaya miki muna iyakar ƙoƙarinmu mu gano inda Ado yake. Za mu sanar da ke da zarar mun samu wani labari mai makama.

**Maman Jamila:** Amma kuma, ranka ya daɗe, abin yana ɗaukar lokaci.

**Yallaɓai:** Bayanin da muka samu shi ne, yana nan ya ɓuya a cikin wannan ƙauyen. Idan har mun tabbatar da gaskiyar hakan, za mu je mu kamo shi.

**Maman Jamila:** To yanzu yaya za a yi da waɗannan yara da suka haddasa mana wannan matsala?

**Yallaɓai:** Na shirya yau da safe zan je na samu Lawan da kuma Zaliha. Amma fa yaran ba su da laifi. A matsayinki na malamar makarata ya kamata ki fahimci cewa ita kanta 'yarki tana da hannu a cikin wannan abin da ya faru.

**Maman Jamila:** Ranka ya daɗe, ita ma Jamila yaudararta aka yi, amma kuma duk da haka ni ce na ɓige da biyan kuɗin asibiti!

**Sakatariya:** Ranka ya daɗe, ku yi haƙuri na katse muku hanzari. Wata mata ce ta zo tana son ganinka.

**Yallaɓai:** Ke ba kya ganin aiki ya yi mini yawa? Wace mata ce wannan?

**Sakatariya:** Cewa ta yi abin da ya kawo ta yana da muhimmanci. Kuma ta ce sunanta Zaliha.

**Yallaɓai:** Zaliha? To ai ita ce matar da nake son gani. Shigo da ita.

**Zaliha:** Salamu alaikum. Ranka ya daɗe, ina kwana? Yaya aiki? … Au Jamila, ke ce a nan? Na ji duk abin da ya faru, amma ban ji daɗi ba. Yaushe aka sallame ki daga asibiti?

**Jamila:** Jiya-jiyan nan, Mama.

**Maman Jamila:** Ka ji munafunci! Kin ma taɓa damuwa ki je duba ta a asibitin ne? Alhalin kuma ɗanki ne ya ja mana duk wannan abin da ya faru?

**Zaliha:** Ɗan tsaya mana? Ke kuwa Maman Jamila, ta ina ɗana ya jawo muku wannan abin?

**Maman Jamila:** Ba ɗanki ne ya je neman rancen kuɗi wajen wannan azzalumin Ado ba?

**Zaliha:** Ki dai faɗi gaskiya! Ko dai ɗan gidan Nana. Don dai ni ɗana bai taɓa ranto kuɗi wurin wannan azzalumin ba!

**Yallaɓai:** Kun ga! Ya isa haka! Kun san kuna cikin caji'ofis!

**Maman Jamila:** Yallaɓai, ai da saura! Wannan matar fa dole sai ta biya ni kuɗin kwanciyar da muka yi a asibiti!

**Zaliha:** Wa kike cewa wannan matar?

**Maman Jamila:** Wace ce kuma in ba ke ba!

**Yallaɓai:** Kai! Na ce ya isa! Ina ganin muna da *'cases'* da yawa a cikin wannan magana. Ina son duk yaran nan da suka

bayyana a gabana yau da rana ina son ganinsu tare da iyayensu. Yanzu ke Zaliha, me ya kawo ki?

**Zaliha:** Ranka ya daɗe, jiya ne waɗansu suka faɗa mini a gida da daddare.

**Mai ba da labari:**

Da jin wannan labari, nan da nan sai jami'in 'yan sandan nan ya bazama. Kafin dai yamma, sai ga shi an kamo 'yan dabar nan a cikin wani lojin da ke ƙauyen.

Da rana ta yi sai ni da Bash da Jamila, duk tare da iyayenmu, muka hallara a caji'ofis inda muka bayyana yadda labarin abin yake tun daga farko! Mun dai baro caji'ofis ne da sharaɗin cewa za mu dinga kai kanmu ofishin a kullu yaumin. Ni saboda na saci rediyon kawuna, shi kuma Bash saboda ya kwaikwayi sa-hannun babansa, ita kuma Jamila saboda ta taimaka mana. Su dai kam iyayenmu duk wannan abin da ake yi, babu abin da suka ce. Wato dai har ya zuwa lokacin da Mama ta fasa ƙwai.

**Fitowa ta 5: A hanyar komawa gida daga caji'ofis da rana**

**Maman Jamila:** Zaliha, ina neman afuwa a kan maganar da na yi ɗazu.

**Zaliha:** Ai ba komai ya wuce, Maman Jamila, kar ki damu.

**Maman Jamila:** Kin san wani lokaci yara kan sa mutane jin kunya.

**Nana:** Ni kaina na ji kunya, ban ji daɗin abin da ɗana Bash ya yi ba.

**Maman Jamila:** Ga shi kullum sai mun faɗakar da su a kan wannan. … Wai Jamila ba ke na nuna wa yadda za ki dinga tattali ba?

**Jamila:** Kin nuna mini, Mama.

**Zaliha:** Kai kuma Ali, ban zaunar da kai na yi maka faɗan cewa ka daina haɗa kanka da sauran mutane ba? Na yi maka ko ban yi maka ba?

**Ali:** Kin yi mini, Mama.

**Zaliha:** To me ya sa kuka jawo mana wannan abin?

**Nana:** Ni wallahi ba na ganin laifinsu, na fi ganin laifin wannan shashashan ɗan nawa.

**Maman Jamila:** Ni ina ganin ya kamata mu koya wa 'ya'yanmu tattali. Mu nuna musu cewa yana da muhimmanci mutum ya dinga ajiye wani kaso na kuɗin da yake samu komai ƙanƙantarsu. Domin idan mutum yana tattali da yawa zai rage kashe kuɗi, kuma zai yi wuya a ce ya fita neman bashi. Ai kun ji abin da nake faɗakar da ku, ko yaran nan?

**Ali/Bash/Jamila:** E, mun ji Mama! Mun gode da wannan shawara.

**Mai ba da labari:**

Babban abin takaicin shi ne cewa, a duk faɗin naihiyar Afirka wannan ita ce matsalar da ta adabi matasa. Kowane matashi za ka tarar yana son mallakar waya mai tsada, da sabuwar kwamfuta, ko kuma tufafin da ake yayi. Amma kuma babban abin da na koya a rayuwata tun ina ƙarami da kuma a wajen wannan aikin bankin da nake yi shi ne, kada mutum ya kuskura ya yi rayuwar da ta fi ƙarfinsa. Babu abin da wannan zai jawo maka illa fitina.

To masu saurare, bari yanzu na koma bakin aikina. Idan kuna son ƙarin bayani a kan wannan shiri, sai ku ziyarci adreshinmu na yanar gizo a

dw.de/lbe. Za kuma ku iya bin shirye-shiryen nan namu a shafinmu na 'Facebook'. Kar ku manta ku kasance da mu a cikin shirin namu na gaba inda zan gaya muku abin da ya faru da Malam Ado, azzalumin mai bayar da bashin nan, da kuma abin da ya faru da Kawu Natanko. Ina fatan kun ji dađin shirin, sai an jima.